# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Daniyel da Atsirin Mafarkin



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Jonathan Hay**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Sarki Nebukadnezar ya yi mafarki, wannan mafarkin ya dame shi sosai.  Ta wurin ikon Allah, Daniyel ya iya fada wa sarki ma’anar mafarkin.**





**Abu na farkon da Daniyel ya yi shi ne ya bayana mafarkin daidai. "Ka ga wani babban siffa na wani gunki, ya Sarki. Siffarsa yana ban mamaki!"**

**“Kan gunkin an yi shi da zinariya,” Daniyel ya ci gaba.**



**“Kirjinsa da kafadarsa an yi su da azurfa.”**



**“Cikinsa da cinyarsa an yi su da tagulla.”**



**“Kafafunsa an yi su da karfe, tafin kafarsa sashi na karfe, sashi kuma laka.”**



**Bayan da bayana gunkin wa sarki,**
**Daniyel ya bi shi zuwa dakin hutu.**



**“Ka duba yadda ake yanka dutse ba tare da hannu ba,” Daniyel ya gaya wa sarki.**



**“Dutsen ya buga siffar a tafin kafarsa mai karfe da laka ya karye kurmus.”**



**“Sa’an na aka nike gunkin ya zama kura aka hura shi ya watse.” Daniyel ya ja aya. “Kuma dutsen ya yi girma zuwa babban tuddu wanda ya cika duniya.”**



**Sarki ya yi mamaki. Daidai abin da ya yi mafarki a kai kenan! Yaya Daniyel ya iya sanin wannan? Saboda Allah ne ya gaya wa Daniyel. Sa’an nan Daniyel ya ci baga da fada wa sarki ma’anar mafarkin.**



“Allah na sama ya baka mulki, iko, karfi, da daukaka,” Daniyel ya gaya wa sarki.  “Kai ne kai na zinariya.”



Daniyel ya gaya wa sarki cewa Mulkinsa na zinariya zai kare. Bangare daya na azurfa na gunkin yana nufin Mulki na 1 marar karfi zai dauki matsayinsa na 2. Tagulan yana nufin wani Mulki na 3. Sa’an nan Karfen da lakan kuma suna nufin Mulki na 4 ne.



**Abu na karshe wanda Daniyel ya gaya wa sarki shi ne: "Allah na sama zai kafa mulki wanda ba za a iya halaka shi ba."**



**Sarki ya fahimta cewa Allah ne kadai wanda zai iya ba wa Daniyel hikiman sani da ganewaa mafarkinsa. Nebukadnezar ya ba da ladan arziki wa Daniyel ya mai da shi mutum mai martaba a mulkinsa.**





**Mulkoki**
**1, 2, 3**
**sun**
**zo sun**
**tafi. Mulkin**
**Allh zai zo**
**bayan na 4.**

**Mai**
**Ceto zi yi**
**mulkia**
**bisan duniya.**
**Kuma ba da**
**daddewa ba!**

**Daniyel da Atsirin Mafarkin**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Daniyel 2**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

32

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**